# Kasuwanci a Intanet

Mahalarta taron za su iya gano wani nau’in bayanin sirri guda ɗaya da za su iya kula da shi ta intanet, wani nau’in bayani guda ɗaya da ba za su iya kula da shi ta intanet ba gaba ɗaya, da kuma wani abu guda ɗaya da za su iya yi game da wani ɓangare na bayanan sirri a intanet wanda ba su ke kula da shi kai tsaye ba.

# Furofayil a Intanet da Bayar da labari

## Kashi na Ɗaya

**Sanar da Ɗalibanka**

Bayanin jama'a da ake da shi game da kai a intanet yana fitowa ne daga wurare da yawa. Za ka iya kula da wasu daga cikin waɗannan wuraren, kamar abun da kake rabawa (misali., hotuna, bidiyoyi, aike mai ɗauke da rubutu) a dandalin sadarwar zamani.

**Tattaunawa a Aji**

Nuna shafin Facebook ɗin Barack Obama a kan allon majigi. Sannan, ka karanta ko ka nuna majigin bayanin da ke nuna naƙasun jawaban da aka samar game da Obama a ƙasa a kan allon majigi. Ka ɗan tabbatar da mahalarta taron sun fahincimci cewa abubuwan da ke cikin waɗannan jawaban da kuma asusun shi kansa almara ce. Sun ƙirƙiri waɗannan ne saboda wannan aikin.

1. @Luciano1782586: Barack Obama na ƙona duk wani abun da ya girka. Har da tattalin arziƙin!

2. @Artemis4062456: Obama ba shi da alƙibla mai kyau. Ya kasa gani hanyarsa ta zuwa White House ba tare da GPS ba!

3. @Sergei5639876: Obama ba zai san manufofin ƙasashen waje ba idan ya jahilci abun.

**Tambayi Ɗalibanka**

Mene ne martaninka ga shafin Facebook ɗin Barack Obama?

Ya batun jawaban da ke nuna naƙasu waɗanda aka danganta su ga Obama?

Yaya kake ganin za su iya sanya Obama ya ji? [misali., ban haushi, cin mutunci.] Kuma yaya za su sanya wasu mutanen su ji wani abu dangane da yanda suke so / suke ƙin Obama?

## Kashi Na Biyu

**Sanar da Ɗalibanka**

Yanzu ka yi tunani game da naka dandalin sadarwar zamani.

**Tambayi Ɗalibanka**

Wane labari ne wanda ya ɗauke hankalin mutane daga karanta furofayil ɗinka?

Wa ya rubuta labarin?

Ta yaya za ka kula da wancan labarin?

Wa za ka iya rinjaya da abubuwan intanet game da kai?

Mene ne ba za ka iya kula da shi ba?

**Sanar da Ɗalibanka**

Duba ɗaya daga cikin bayanan sirrinka na furofayil ɗin dandalin sadarwar zamani (Facebook, Instagram, Snapchat, Twitter, Wechat, da dai sauransu.) ko furofayil ɗin dandalin sadarwar zamanin wani fitaccen mutum (misali., wani a cikin mawaƙa da / ko masana'antar fim [fina-finai / TV], fitaccen ɗan siyasa, babban ɗan kasuwa. Zaɓi abubuwa da yawa (misali., hotuna, bidiyoyi, aike masu ɗauke da rubutu) da ake gani a kan furofayil.

**Tambayi Ɗalibanka**

Wa ya ƙirƙiri aiken? Me yasa?

Mene ne wasu daga cikin jawaban?

Wa ake so a cimma da kowane aiken?

Wane bayani ne ya rage?

# Aiki

## Aiki

### Aiki

Nemi mahalarta taron su rubuta wasu ‘yan sakin layi dangane da aiken da suka sake dubawa a cikin ayyukan da suka gabata sannan su amsa tambayoyin da ke tafe:

Wane nau’in abu ne guda ɗaya da kai/wanda ya mallaki asusun ke YI/YAKE YI a wajen kula?

1. Amsoshin da aka bayar da shawara: naka sunan mai amfanin; naka matsayin da aka sabunta; aikenka / abubuwan da ka raba / tweets; hotuna ko bidiyoyin da ka loda a labaranka ko abubuwan tunawarka; jawaban da ka yi a kan abun da wasu mutanen suka raba a dandalin sadarwar zamani.

Wane nau’in abu ne guda ɗaya da kai/wanda ya mallaki asusun BAI YI/BA YA YI a wajen kula?

1. Amsoshin da aka bayar da shawara: jawaban da wasu mutane suka yi a kan jawaban da ka raba a dandalin sadarwar zaman (misali., labaranka, abubuwan tunawa, sabunta matsayi, tweets), abubuwan da wasu suka raba a dandalin sadarwar zamani, yanda abokai / mabiya / waɗanda aka haɗa ka da su don raba abubun da ka loda a intanet.

Mene ne abu guda ɗaya da za ka iya yi dangane da wani abun da wani ya rubuta game da kai da ba ka so saboda wasu dalilai (ma’ana., Ba kai ba ne kake kula da wannan bayanin kai tsaye ba)?

1. Amsoshin da aka bayar da shawara: cire maƙalawar da aka yi maka; tuntuɓi mutumin da ya raba abun sannan ka nemi su cire shi; cire mai yin amfanin; idan kana jin tsoron lafiyarka, sanar da wani babban mutun da ka amince da shi; ya danganci dandalin sadarwar, za ka iya kai ƙarar abun sannan / ko mai yin amfanin idan yana damun ka ko wuƙantawa.

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarƙashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarƙashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein.